# ZURI’AR HAMBALAWA DA ALQALANCI

## TAQAITACCEN BAYANI A KAN DARAJA DA MUHIMMACIN SHARI’AH DA ALQALANCI; DA BAYANI A KAN ZURI’A MAI KIMANIN SHEKARU 300 SU NA ILMANTARWA DA YIN ALQALANCI A QASAR HAUSA


**Daga**

**Professor Sani Abubakar Lugga, MFR**

**The 5th Waziri of Katsina**

Doctor of Management Studies (Doc.Mngt);
Doctor of Philosophy in Conflict Management (PhD);
Fellow of the Nigerian Institute of Management (Nigeria);
Fellow of the Institute of Management Consultants (Nigeria);
Fellow of Institute of Professional Financial Managers (UK);
Fellow of Institute of Journalism and Management (Nigeria);
Fellow of the Chartered Institute of Commerce of Nigeria;
Fellow of the London Graduate School (United Kingdom);
Ambassador of Universal Peace Federation (New York);
Member of Professors World Peace Academy (Korea);
Visiting Professor at Ecole Surperieure Universitaire
(Bi-lingual University) Cotonou, Republic of Benin;
Consultant to the National Council of
Traditional Rulers of Nigeria.



19th Jumadal Ula 1445 AH
3rd December 2023 AD

بسم الله الرحمن الرحيم

نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين

Mai Girma Shugaban Taro, Hon. Justice Umaru Abdullahi, Walin Hausa kuma Shettima Ilmuye na Borno

'Ya'yan Zuri'ar Hambalawa

**Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta'ala wa Barkatuhu.**

Ina mai godiya ga Allah (SWT) da Ya qaddara saduwarmu a yau wajen wannan taro mai muhimmanci. Ina farin ciki da wannan Zuri'a mai albarka ta ga ya dace in zo domin in yi taqaitaccen bayani a kan abin da Allah Ya sanar da ni game da Zuri'ar Hambalawa da irin tasirin da suka yi wajen koyo da koyar da Addinin Musulunci da kuma tsare Shari'ar Allah (SWT) ta hanyar Alqalanci na tsawon kusan shekaru 300 a Qasar Hausa da sauran Najeriya baki xaya.

Wasiqar da kuka aiko mani da harshen Turanci ta bukaci in yi jawabi kan "HAMBALAWA AND THE JUDICIARY", watau "Hambalawa da Alqalanci". Kuma Wasiqar ta bani dama in yi ma wannan maudu'i kwaskwarima gwargwadon yadda na ga ya dace. Don haka na ga ya dace inyi wannan jawabi nawa cikin harshen Hausa kuma, insha Allah, zan yi bayanai a wannan qasida kamar haka:

1. Ina sane da cewa wasu masana a cikin Zuriar ku sun yi rubuce-rubuce da dama a kan tarihin ku, musamman a kan ayyukan Alqalanci da sauran fannonin ayyuka da kuka yi. Sun kuma yi taqaitaccen bayani a kan tushen Zuri'ar ku da

lissafi a kan kakanni da iyaye da ‘ya’ya da jikoki na wannan Zuri’a. Don haka ba zan bayar da muhimmanci ba a kan waxannan.

2. Zan bayar da muhimmanci a akan yin bayanai game da abin da ban ga an rubuta ba na asalinku da irin tasirin da kuka yi na tsawon kimanin shekaru 300 kuna koyon ilmin Addinin Musulunci kuma kuna koyar da shi. Sannan kun tsare wannan Addini ta yin Alqalanci a bisa Shari’ar Musulunci da kuma ta Zamani. Na yi wannan ne domin na fahimci cewa wannan Zuri’a ta Hambalawa ta yi shekaru kimanin 300 kamar yadda Zuri’ar mu ta Waziri Haruna bana tana da shekaru 444 a cikin ayukan Jihadi, Mulki da ilmin Addinin Musulunci. Wannan ya nuna cewa babu wata Zuri’a a Katsina da ke da irin wannan tarihi kuma babu wata Zuri’a a Katsina mai yawan jama’a kamar waxannan Zuri’oi guda biyu.

3. A bisa haka, insha Allah, zan yi bayanai a kan Shari’ah da banbancinta da Sasantawa ko Sultuntawa. Kuma zan yi bayanai a kan asalinku tun daga Futa Jallon har zuwa Qasar Gobir da Garuruwan Sifawa da ‘Yan-Doto a Qasar Zamfara har zuwa Garin Makurxa da Birnin Katsina a cikin Qasar Katsina. Zan kuma tava kaxan daga cikin gudummuwa da wanna Zuri’a ta bayar wajen Jihadin Sheikh Usman Danfodiyo da kuma fannin Ilmin Addinin Musulunci da Alqalanci.

## MENE NE SHARI’AH, SASANTAWA KO YIN SULHU?

Shugaban Taro, ‘Yan Zuri’ar Hambalawa;

Ba shakka dukkan ku kuna alfahari da cewa kun fito daga Zuri’a mai albarka ta Alqalai, amma ‘yan kaxan ne cikin ku suka

yi ko suke yin Alqalanci saura kuma sun shahara a fannoni na ayyukan rayuwa iri-iri. Amma yana da muhimmanci ku san abubuwan da suka shafi asalin ku na Alqalanci, domin ana wasa da Shari'ah da Alqalanci duk da cewa ya shafi rayuwa, ba ta Musulmi kaxai ba, a'a, har ma duk mahaluqai baki xaya, daga Mutane zuwa Aljannu da dabbobi da sauran halittu masu rai. Amma bayananan da zamu yi a nan su ne waxanda suka shafi Mutane, 'ya'yan Annabi Adam (AS).

Tun lokacin da Allah Ya saukar da Annabi Adam (AS) da Hawwa'u daga al-Janna zuwa wannan Duniyar, kuma suka fara haihuwar 'ya'ya, sai fafutukar yadda za'a tsara rayuwa ta shigo. Ana nan ana ta fama da wannan mas'ala tsawon shekaru aru-aru, sai Allah (SWT) Ya bayar da tsari na qarshe, watau tsarin Shari'ar Musulunci.

**Mene Ne Ma'anar "Shari'ah?"**

A taqaice, **Shari'ah** tana nufin hanya ko tsari na rayuwar Musulmi. Kuma an samo wannan tsari ne daga al-Qur'ani mai Tsarki da Sunnar Annabi (SAW) da Ijma'i ko Qiyasi na Malaman Sunnah. Shari'ah ta shafi rayuwar Musulmi kaf, tun daga xaukar ciki har ya zuwa haihuwa har renon yara har girman mutum har yadda zai yi mu'amalla har zuwa mutuwar shi da yadda za'a rufe shi a qabari. Don haka, Shari'ah ita ce rigar Musulunci domin Musulunci ya shafi rayuwar Musulmi daga haihuwa zuwa mutuwa, watau abinda Turawa ke kira "*from the cradle to the grave*".

**Rassan Shari'ah**

Daga cikin tsarin Shari'ah, ana iya fitar da rassa ko kasusuwa biyar kamar haka:-

1. Kashi na farko ya danganci bautar Allah (SWT) (watau ***ibadat***) kamar Sallah, Zakka, aikin Hajji da makamantan su. A zamanin yanzu ba'a zuwa wurin Alqali ko Sarki ko wani mai hukunci a waxannan nau'oin ibada sai dai a yi ma wanda ke wulakanta su nasiha.
2. Kashi na biyu ya danganci huxxa tsakanin mutane (watau ***mu'amalat***) wadda rikici ko jayayya kan faru. A nan ana zuwa wurin Alqali ko wurin sauran mahukunta domin warware rikicin ko jayayyar. Watau **Shari'ah** ta shigo
3. Kashi na ukku ya shafi laifuffuka waxanda za su jaza hukunta wanda ya aikata su kamar yin zina, sata, shan giya da makamantan su. A nan ma **Shari'ah** ta shigo.
4. Kashi na huxu ya shafi inda wani ko wasu mutane su kan sasanta ko su yi sulhu tsakanin masu jayayya ba tare da zuwa gaban Alqali ba. A nan **Sasantawa** ta shigo (watau kamar a ce Mallam Abubakar ya sasanta tsakanin Mallam Umar da Mallam Usman).
5. Kashi na biyar ya danganci yin sulhu wanda masu jayayya za su yi ba tare da zuwa wurin kowa ba. A nan yin **Sulhu** ya shigo (watau kamar a ce Mallam Abubakar da Mallam Usman sun yi sulhu da junan su, ba tare da wani ya shiga tsakani ba).

**<u>Tushen Shari'ah</u>**

Tushen Shari'ah yana nufin hanyoyin da aka samo hukunce-hukuncen Shari'ah, watau "***Sources of Islamic Law"*** da harshen Turanci.

Tun lokacin da Musulunci ya shigo qasar Hausa wajen shekarar 1100 Miladiyya, mutanen wannan sashe na Duniya suka fara aiki da Shari'ah. Musuluncin kuma ya shigo qasar

Hausa ne ta Daular Kanem-Bornu wadda ita ta samu Musulunci tun wajen shekarar 800 Miladiyya ta hanyar cinikin Ratsin Sahara, watau “Trans Saharan Trade”. Shehunnan Daular Kanem-Bornu sun yi Jihadi na shekaru xaruruwa wajen Jaddada Musulunci hat ya yaxu tun daga Fezzan a Libya har zuwa qasashen Hausa da Nupawa da Yarabawa. Jihadin da Shehu Usman Danfodiyo ya yi ma jagoranci a shekarar 1804 miladiyya ya qara jaddada amfani da Shari’ah. Lokacin da Turawan Ingilishi suka gabatar da mulkinsu na danniya a sabuwar qasar da suka qirqira mata suna “Nigeria” a shekarar 1914 miladiyya, sai suka kawo canje-canje a halin rayuwar jama’a. Amma duk da wannan tilas suka bar Shari’ah tana aiki a qasashen Arewacin Najeriya musamman abin da ya shafi aure, gado, ibada, zamantakewar iyali da sauransu.

Turawa sun kawo wani sabon salo na yin dokoki domin ayyukan gwamnati. A nan ne suka saqa ‘yan gyare-gyare a kan yadda ake tafiyar da mulki ta hanyar Musulunci a Arewacin Najeriya. Lokacin da Turawa zasu bayar da mulkin kai a shekarar 1960 miladiyya sai suka tilasta kawo wani tsari na Shari’ah mai suna **“penal code”.** Watau aka yi ma Shari’ar Musulunci wani kundi wanda ya gabatar da hukunce-hukunce akan laifuffuka iri-iri. Abinda ya shafi zamantakewar iyali (**personal law**) an bar shi kamar yadda Musulunci ya shimfixa amma aka yi ‘yan canje-canje wajen abinda ya shafi karya dokoki da laifuffuka (**criminal law).**

Tun wancan lokaci ne Musulmi ke neman a koma ma Shari’ah kamar yadda Allah ya shinfixa, amma wannan bai samu ba sai a shekarar 1999 miladiyya inda Allah Ya hukunta wasu Jihohin Najeriya da Musulmi sukafi yawa ko rinjaye suka koma ma tsarin Allah.  A waxannan Jihohi, an yi dokoki da suka jaddada

yin amfani da Shari’ar musulunci a kan Musulmi, kamar yadda Allah Ya shar’anta. Dukkan dokokin da Jihohin suka kafa sun bayyana cewa duk mai yanke hukunci ko sasantawa ko yin sulhu a Musulunce, to, tilas ne ya yi amfani da littattafai da sauran fannoni na Shari’ah. A cikin sashe na IV, qaramin sashe na 8, na Doka mai Lamba **CAP.173**, wadda ta mayar da amfani da Shari’ar Musulunci a Jihar Katsina, an bayyana shika-shikai guda shidda (6) waxanda dukkan Malaman Islama na Duniya suka yarda da cewa su ne “Tushen Shari’ah”. Ga waxannan shika-shikai guda shidda tare da xan bayani a kan ko wanen su**:-**

1. **Al-Qur’ani Mai Tsarki:** Tilas ne Mai Hukunci ya san nassin al-Qur’ani da inda ya kamata a fitar da hukunci da abinda hukuncin ya qunsa. A nan ya wajaba ya san tafsiri da sharuxxan da suka shafe shi.

2. **Hadissai da Sunnonin Manzon Allah (SAW):** A nan ma wajibi ne Mai Hukunci ya san Hadissai da Sunnonin Manzon Allah (SAW) kuma ya san inda zai ajiye ko wanen su da irin ruwayar da aka yi da ingancin ruwayar ko rashin ingancin ta.

3. **Ijma’i (haxuwar Malamai):** Wajibi ne Mai Hukunci ya ilmantu a kan ijma’i ko haxuwar Malamai a kan nassin Al-Qur’ani ko Hadissai ko Sunnonin Manzon Allah (SAW). Duk abinda Malamai suka amince kuma suka haxu a kan shi, ya zama abin yin hukunci da shi.

4. **Qiyas (qiyasi ko kwatanta wani abu da wani abun wajen yin hukunci):** Mai Hukunci tilas ya san hukunce-hukuncen da aka yi a gabanin shi kuma ya san yadda zai kamanta mas’alar da ta zo a gaban shi da waxannan hukunce-hukunce. Shi ma lallai ya laqanci yadda zai yi qiyasin mas’alolin da aka kawo a gaban shi, waxanda ba su da hukunci

a kai tsaye. Watau sai ya kamanta su da wasu hukunce-hukuncen da suka yi kama da su waxanda ke cikin al-Qur'ani ko waxanda aka samo daga cikin Sunnar Annabi (SAW).

**5. Ijtihad (ijtihadi ko fatawar Malamai ko wani Babban Malami):** A nan ana son Mai Hukunci ya san fatawar da aka yi a kan wata mas'ala wadda ba'a jingina ta da ijma'in Malamai ko qiyasi ba.

**6. Al-Urf (al-ada wadda bata sava ma Musulunci ba):** Duk Mai Hukunci lallai ya san al-adun jama'ar sa kuma ya san waxanda ba su sava ma Musulunci ba da waxan da suka sava domin gudun hallata haram, ko haramta halal.

**A lura cewa:-** Za'a fara duba hukuncin ko wace irin mas'ala da ta faru a cikin Al-Qur'ani Mai Tsarki, idan ba'a samu hukunci ba, sai a duba Hadissai da Sunnonin Manzon Allah (SAW), sannan sai Ijmah, sannan sai Qiyas, sannan sai Ijtihad, sannan sai Al-Urf. Ana kuma iya harhaxa su domin a samu ingantaccen hukunci.

**A kuma lura cewa:-** Ba zai yuwu wani ya samu wadataccen ilmin shika-shikan nan guda shidda ba, sai idan yana da cikakken ilmin harshen Larabci. Watau tilas ya san Nahawu da Balagar harshen Larabci, domin yawancin tafsiran Al-Qur'ani da tarjamomin littattafan Fiqihu daga harshen Larabci zuwa wasu harsuna (kamar Hausa ko Yarabanci ko Turanci ko Faransanci) ba zasu wadatar ba.

**Mene Ne Sulhu?**

Yin Sulhu wani nau'i ne na Shari'ah inda mutane ke daidaita tsakanin su a kan wata mas'ala da ta shafi haqqoqin su ba tare da sun je gaban Alqali ba. Abin lura shi ne, ana yin Sulhu ne a

kan abin da ya shafi haqqoqin mutane amma ba a kan abin da ya shafi haqqoqin Allah ba, watau ba'a yin Sulhu akan abin da ya shafi laifuffuka waxanda za su jaza hukunta wanda ya aikata su, kamar yin zina, yin sata, shan giya da makamantan su. A nan tilas sai an yi Shari'ah a gaban Alqali domin shi kaxai ke da ikon yin haddi ko yin hukuncin da ya dace. Allah (SWT) Ya inganta yin Sulhu inda Ya ke cewa,

[illegible]

*Babu laifi garesu idan suka daidaita yin ingantaccen sulhu tsakanin su; domin yin sulhu shi ne mafi alheri* (Suratun Nisa'i: 128)

Manzon Allah (SAW) ya jaddada amfanin yin Sulhu inda Tirmizhi ya ruwaito Hadisin Annabi (SAW) ya ke cewa,

**الصُّلْحُ جَائِزٌ بَيْنَ الْمُسْلِمِينَ إِلاَّ صُلْحًا حَرَّمَ حَلاَلاً أَوْ أَحَلَّ حَرَامًا وَالْمُسْلِمُونَ عَلَى شُرُوطِهِمْ إِلاَّ شَرْطًا حَرَّمَ حَلاَلاً أَوْ حَلَّ حَرَامًا.**

*Sulhu ja'izi ne a tsakanin Musulmi, sai fa sulhun da ya hallata haram, ko ya haramta halal. Kuma idan Musulmi suka sanya wani sharaxi tsakanin su, to suna nan kan wannan sharaxi, sai fa sharaxin da ya halatta haram ko ya haramta halal.*

Sheikh Abubakar ibn Asim al-Gamadi al-Andulusi mawallafin littafin da ya fi ko wane shahara a fannin Shari'ah a mazhabar Malikiyya, watau *Tuhfatul Hukkam* ya yi bayanin Sulhu a shafi na 137 (fassarar Alqalin Alqalai Usman Muhammad Daura) haka:-

*Dukkan Malamai sun haxu a kan halaccin yin sulhu, a kan iqirari ko akan inkari, idan ya zama an yi shi a kan yardar masu yin Sulhu xin, ba tare da an tilastawa wani ba. Kuma yin Sulhu kamar ciniki ya ke, duk abin da ya halatta a wajen ciniki ya*

*halatta a wajen Sulhu; kuma abin da ya haramta a wajen ciniki ya haramta a wajen Sulhu.*

Ana iya fahimtar amfanin yin sulhu idan aka yi la'akari da cewa:-

1. Duk wanda ya kai wani a gaban Alkali, to, ya haddasa rashin jituwa wadda ke da wuyar warwarewa kuma irin wannan rashin jituwa ta kan zamo wadda ke shafar 'ya'ya da jikoki.
2. Zuwa kotunan Alkalai, musamman a wannan zamani, su kan jawo kashe kuxaxe ta hanyar zirga-zirga da wani lokacin ma biyan kuxaxen Lawyoyi da wasu hidimomi makamatan waxannan.

**<u>Mene Ne Sasantawa?</u>**

Sasantawa ko yin Sasanci wani nau'i ne na Shari'ah inda wasu amintattun mutane (kamar Sarakuna, Manyan Malamai ko Dattawan da ake girmamawa) ke daidaita tsakanin wasu mutane a kan wata mas'ala da ta shafi haqqoqin mutanen ba tare da an je gaban Alqali ba. Abin lura shi ne, ana yin Sasanci ne a kan abin da ya shafi haqqoqin mutane amma ba a kan abin da ya shafi haqqoqin Allah ba, watau ba'a yin Sasanci akan abin da ya shafi laifuffuka waxanda za su jaza hukunta wanda ya aikata su, kamar yin zina, yin sata, shan giya da makamantan su. A nan tilas sai an yi Shari'ah a gaban Alqali domin shi kaxai ke da ikon yin haddi ko yin hukuncin da ya dace.

Ya kamata a jaddada cewa, tilas ne masu Sasanci su san hukunce-hukuncen Shari'ah a kan halalci ko haramcin ko wace mas'ala da za su yi sasanci a kan ta. Misali, halal ne a saurari kuma a sasanta masu mas'alar aure amma haram ne a saurari ko a sasanta masu mas'alar sata ko zina ko liwaxi. Idan mutane suka zo da mas'alar sakin aure ko renon yara ko kula

da dukiyar su, to wajibi ne a saurare su kuma a yi duk abin da za' a yi domin sasanta su. Wannan zai gyara zumunci da zamantakewa maimakon a je wajen Alqali inda zumunci zai iya lalacewa. Amma idan aka zo da mas'alar yin luwaxi ko zina, to haram ne a amshi wannan mas'ala har a kira wanda ake tuhuma da laifin domin ba'a sasanci a mas'alar da ke da yin haddi a cikinta. Wannan aikin Alqali ne.

Wani dalilin kuma da ya sa ba'a sauraren irin wannan mas'alar shi ne, gudun tozarta wanda ake zargi domin mutane za su yi ta ganin mutumen da ake zargin da fuskar fasiqi, ko da an kasa tabbatar da zargin. Kuma idan an kasa kawo shaidu guda huxu, to sai an hukunta waxanda suka kawo maganar domin yin qazafi da suka yi.

Ya kuma kamata a jaddada cewa, a Musulunci, ba'a yin Hukunci ko Sasanci, kai, ba'a yin komai, sai da ilmi. Idan waxanda aka zo wurinsu domin yin sasanci basu da ilmin da ya dace da yin sasancin, to sai su nemo ma'abota ilmi domin su taimaka. Allah (SWT) Ya ce,

*Ku tambayi ma'abota sani idan ku ba ku sani ba* (Qur'an, 16:43 da kuma 21:7).

**Akwai Banbanci Tsakanin Sulhu Da Sasantawa?**

A harshen Hausa, ana yawancin amfani da kalmomin "Sulhu" da "Sasantawa" a matsayin ma'ana guda, amma wani lokaci akan banbanta wajen amfani da su. Misali, a kan ce, "mun yi sulhu tsakanin mu", ko "mun sasanta tsakanin mu", kuma wannan ya xauki ma'ana guda. Amma ba a kan ce, "Hakimi ya sulhunta mu" ba, sai dai a ce, "Hakimi ya sasanta mu".

Watau, duk da ma'anar kalmomin kusan xaya ce, a kan yi amfani da kalmar "sulhu" idan mutane suka daidaita tsakanin su ba tare da zuwa wurin wani mai shiga tsakani ba. Kuma akan yi amfani da kalmar "sasantawa" idan wani ya shiga tsakani, watau ya sasanta su ke nan.

## SIFOFIN ALQALAI DA MASU SASANTAWA

A dubi darajar da Allah Ya ba Alqalai tun zamanin Annabawa (AS) da Sahabbai (RLA). Misali, a zamanin Sayyidina Umar (RLA), wanda ni a gani na, ba'a yi Shugaba mai adalci ba kamar shi tun daga wancan lokacin har ya zuwa yau, an kai shi qara gaban Alqalin da shi ya naxa shi, kuma ya amince da hukuncin da aka yi wanda shi Sayyidina Umar (RLA) bai yi rinjaye ba.

Kuma a duba a yau, duk faxin Duniyar nan, daga Talaka har zuwa Shugaban Qasa, wanda duk Alqali ya hukunta shi, to ya hukuntu ke nan. To, a Najeriya, hukuncin Alqalan Kotu ne ke tabbatar da duk Zavavvun Mutane daga Kansila har zuwa Shugaban Qasa. Zave, da Hukumar Zave duk basu da ikon da Alqalai suke da su. Ashe wajibi ne Alqalai su zamo masu ingantattantun sifofi.

A matsayin mu na Musulmi, Musulunci ya shar'anta cewa wanda duk Allah (SWT) Ya aza ma nauyin yin **HUKUNCI** ko **SASANTAWA** tsakanin mutane, watau Sarki ne ko Alqali ne ko wani Shugaba ko wani Dattijo da jama'a suka buqaci ya sasanta su, to lallai ya zamo mai ilmi a bisa abinda aka buqace shi ya yi hukunci ko sasasantawa a kai. Kuma ya yi wannan hukunci ko sasantawa da adalci. Idan bai da ilmi a kan mas'alar, to tilas ya kira mai ilmi ko ya aika masu buqatar hukuncin ko sasantawar zuwa ga mai ilmin. Wannan ne zai

sanya duk wanda Allah (SWT) Ya aza ma nauyin hukunci ko sasantawa ya sauke nauyin kuma Al-Jannah ta zama makomar shi a Lahira.

Ko da mutane ne suka amince za su yi sulhu tsakanin su ba tare da zuwa wajen kowa ba, tilas ne su san hukunce-hukuncen da suka shafi abubuwan da za su yi sulhu a kan su. Idan ba su da ilmin yin haka, to tilas ne su kira mai ilmi ya jagoranci yin sulhun.

**<u>MATASHIYA</u>:-**

Sifofin masu yin hukunci a Kotu (watau Alqalai) da na masu sasanta mutane duk xaya ne, domin duk waxannan ayyuka ana yin su ne a bisa ilmi**.** Watau da Alqalai da masu sasanta mutane tilas ne su yi bincike, su amshi shaidu kuma su yi duk abinda Musulunci ya shinfixa domin tabbatar da mai gaskiya domin yanke HUKUNCI ko yin SASANCI a bisa adalci. Sai da ilmin yin wannan aiki ne za'a iya gano mai haqqi kuma a bashi haqqin sa, domin samun sasantawa ko yin sulhu mai xorewa kuma yadda Allah Ya amince a yi.

**<u>Masu Hukunci Iri Ukku Ne, Xaya Ya Na Aljannah Biyu Su Na Wuta</u>**

Sheik Abubakar ibn Asim al-Garnadi al-Andulusi yana xaya daga cikin manyan Alqalan Musulunci da aka tava yi a faxin duniyar nan, kuma ya rayu a qasar Andalus (watau Spain ta yanzu) a zamanin da qasar take qarqashin mulkin Islama. Ya rubuta littafi a kan Shari'ar Musulunci wanda babu kamarsa a qasashen Afirka ta Arewa da ta Yamma (watau North and West Africa) kuma yana cikin manyan littattafan da ake amfani da su a nan qasashen Najeriya da Nijar da sauran maqwabta. Wannan littafi mai suna "***Tuhfatul Hukkam***" watau wanda

marigayi Alqalin Alqalan Jihar Katsina, Alhaji Usman Muhammad Daura, ya yi ma tarjama da sunan, **“Jagorar Masu Hukunci”**, Sheik ibn Asim ya wallafa shi ne a shekarar 820 Hijrah (watau fiye da shekaru 600 da suka wuce) kuma har yanzu ana taqama da shi. A tarjamar littafin da marigayi Alqalin Alqalan Jihar Katsina, Sheik Usman Muhammad Daura ya yi, an faxa a Baitocin farko (watau Baiti na 11 zuwa na 13) cewa:-

*Ina roqon Ubangiji, Ya yi mani sauqi*
*ga abin da ya xora mani na hukunci.*
*Kuma ina roqon Shi dauriya da katari, don in zamo*
*daga cikin jama’ar da suke yin adalci da gaskiya.*
*Har in zamo* ***xaya*** *daga cikin Alqalai ukku,*
*Aljannar Firdausi ta zama makoma gare ni.*

Sheik ibn Asim al-Garnadi ya buxe littafin shi da waxannan baitoci ne domin ishara da Hadisin da An-Nasa’i ya ruwaito Abu Huraira (RA) ya na cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce,

**الْقُضَاةُ ثَلاَثَةٌ اثْنَانِ في النَّارِ وَوَاحِدٌ في الْجَنَّةِ رَجُلٌ عَرَفَ الْحَقَّ وَقَضَى بِهِ فَهُوَ في الْجَنَّةِ وَرَجُلٌ عَرَفَ الْحَقَّ فلم يَقْضِ بِهِ وَجَارَ في الْحُكْمِ فَهُوَ في النَّارِ وَرَجُلٌ لم يَعْرِفْ الْحَقَّ فَقَضَى لِلنَّاسِ على جَهْلٍ فَهُوَ في النَّارِ.**

*Masu hukunci guda ukku ne, biyu suna wuta xaya kuma yana Aljannah. Wanda ya san gaskiya kuma ya yi hukunci da ita, wannan yana Aljannah. Wanda ya san gaskiya amma bai yi hukunci da ita ba, ya yi zalunci, wannan yana wuta. Wanda bai san gaskiya ba, ya yi ma mutane hukunci a kan jahilci da son ran shi, wannan yana wuta.*

## <u>Ilmin Da Ya Kamaci Mai Hukunci</u>

Sheik ibn Asim al-Garnadi ya bayyana sifofin wanda ya kamata ya yi hukunci a Musulunci a Baitoci na 14 zuwa 17 kamar haka:-

*Mai zartar da hukunce-hukunce a bisa fuskar Shari'ah,*
*Shi wakilin Khalifa ne.*
*An so rashin tsoro ga Mai Hukunci kuma*
*Sharaxin shi balaga da adalci.*
*Kuma ya zamo namiji, xa, kuvutacce daga rashin*
*Gani, da rashin, ji da rashin magana.*
*An so cikakken ilmi ga Mai Hukunci, da tsantseni,*
*Kuma ya san Hadisi da Fiqhu.*

A cikin sharhin shahararren littafin Fiqhu na Sheik Abdur-Rahman ibn Muhammad ibn Askar al-Bagdadi mai suna ***Irshad Al-Salik*** wanda aka fi sani da sunan ***Askari,*** an bayyana sifofin Mai yin Hukunci a Musulunci a shafi na 471 kamar haka:-

1. Lallai ne ya zama Musulmi.
2. Mai hankali
3. Baligi ba yaro ba
4. Namiji ba mace ba
5. Xa ba bawa ba
6. Ya kasance yana da lafiya ta ji, da ta kwakwalwa, da ta gani da ta harshe, wato maganar shi tana fita sosasi
7. Ana so Mai Hukunci ya zamo Malami, masani wanda ya kai darajar *Mujtahidi*. Watau wanda ya san abin da ya shafi hukunce-hukuncen Shari'ar Musulunci a cikin Alqur'ani da Sunnah. Kuma ya san Nassi Ammi, Mujimali, Mubayyani, Nasihi da Mansuhi na Alqur'ani. Kuma ya san Mutawatir, Ahada, Mutasili, da Mursali na Sunnah. Ya kuma san halayen masu ruwayar Hadisi wajen karfin su da raunin su. Kuma ya san harshen Larabci, Nahawun sa da Balagar sa. Kuma ya iya tace maganganun Sahabbai (RA) da na waxanda suka

biyo bayan su. Ya kuma gane inda suka dace da juna da inda suka yi savani. Ya kuma san Qiyasi da nau'oin sa.

Wanda duk Allah (SWT) Ya aza ma nauyin yin hukunci, walau Alqali ne ko wani Shugaba ko wani Dattijo da jama'a suka buqaci ya sasanta ko ya sulhunta su, to lallai ya zamo mai ilmi a bisa abinda aka buqace shi ya yi hukunci ko sasasantawa ko sulhuntawa akai. Kuma tilas ne ya yi wannan hukunci ko sasatanwa ko sulhuntawa da adalci.

**<u>Me Ya Kamata Mai Sulhuntawa Ko Sasantawa Ya Yi</u>?**

Fiye da shekaru 1,000 aka yi, Sarakuna da Alqalan da ke qarqashin suna yin Shari'ah a wannan sashe na Duniya. Watau wuraren da Musulmi su ke da rinjaye a Afrika ta Yamma. Wannan tsari ya xore har 1967 miladiyya a Najeriya, watau lokacin da Gwamnatin Tarayya ta amshe harkar Shari'ah da Kotuna da 'Yan-Sanda da Kurkuku daga hannuwan Sarakuna ta mayar da su a qarqashin ikon Gwamnati. Duk da wannan, jama'a basu bar zuwa wajen Sarakuna ba, domin **Sasantawa** ko yin **Sulhu** tsakanin su a kan mas'alolin rayuwa.

Kamin a amshe harkar Shari'ah daga hannun Sarakuna, a Majalisar ko wane Sarki akwai masu ilmi a kan Shari'ah kamar Muhuti, (watau *Mufti* mai yin *fatwa*), da Alqalin Garka (watau Alqalin Majalisa) da Liman (watau Limamin Juma'a) da Wali (watau masani a kan Shari'ah). Wannan ya nuna cewa wajibi ne Sarakuna da 'Yan-Majalisun su da Malamai da Iyaye da Dattawa da sauran waxanda jama'a ke zuwa wurin su domin yin sulhu a **wannan zamanin**, su san qa'idoji da sharuxxan yin sulhu, domin guje ma "***hallata haram, ko haramta halal",*** kamar yadda Tirmizhi ya ruwaito Hadisin da Manzon Allah (SAW) ya ke cewa,

« الصُّلْحُ جَائِزٌ بَيْنَ الْمُسْلِمِينَ إِلاَّ صُلْحًا حَرَّمَ حَلاَلاً أَوْ أَحَلَّ حَرَامًا وَالْمُسْلِمُونَ عَلَى شُرُوطِهِمْ إِلاَّ شَرْطًا حَرَّمَ حَلاَلاً أَوْ حَلَّ حَرَامًا ». رواه الترمذي

*Sulhu ja'izi ne a tsakanin Musulmi, sai fa sulhun da ya hallata haram, ko ya haramta halal. Kuma idan Musulmi suka sanya wani sharaxi tsakanin su, to suna nan kan wannan sharaxi, sai fa sharaxin da ya halatta haram ko ya haramta halal.*

**A lura:-** Abin fahimta a nan shi ne, duk wanda aka kawo ma wata mas'ala domin ya yi hukunci ko sasantawa ko sulhuntawa, kuma bai da ilmi a kan mas'alar, to sai ya kira mai ilmi ko ya aika masu bukatar hukuncin ko sasantawar ko sulhuntawar zuwa ga mai ilmin. Bayan ya yi haka, sai kuma ya sanya ido ya tabbatar da cewa an yi adalci a kan al'amarin. Misali, idan aka zo wajen wani Shugaba da wata mas'ala sai ya bi waxannan matakan:-

1. Ya saurari masu koke da irin koken da suka zo da shi.
2. Idan abin da zai iya sasantawa ne a kai kuma masu koken sun gamsu da sasancin, to, sai ya sasanta.
3. Idan abin ya shafi hukumar 'Yan Sanda ne, to, sai ya aika su wajen 'Yan Sanda kuma ya bi kadin maganar domin a yi adalci a kan ta.
4. Idan abin ya shafi Kotuna ne, to, sai ya aika su wajen Alkali kuma ya bi kadin maganar domin a yi adalci a kan ta.

Wanda duk ya yi haka, to, ya taimaka ma masu mas'alar kuma ya taimaka ma 'Yan Sanda da Alkalai domin ba za su yi wasa da maganar ba tun da ta fito daga wajen wani Shugaba ne kuma sun ga Shugaban ya sanya idanu a kan ta. Wanda duk ya aikata haka, kamar ya yi aikin ne da kan shi bisa ilmi, kuma sakamakon shi na nan kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya ce,

« الدَّالّ عَلَى الْخَيْرِ كَفَاعِلِهِ ».

*Wanda duk ya shiryar aka yi aikin alheri, to ladar shi kamar ta wanda ya aikata alherin da ya shiryar aka aikata.*

# ASALIN HAMBALAWA

Duk rubuce-rubucen da na gani akan Zuri'ar Hambalawa, an haxu da cewa daga tsatson Sheikh Muhamammadu Shumo su ke wanda aka ce ya zo Qasar Hausa tare da Mahaifin Sheikh Usman Danfodiyo, watau Sheikh Muhammad Fodiyo, kuma suka fara zama a Birnin Sifawa wadda ke Jihar Sokoto a yau. An kuma ce sun zo Sifawa ne daga Qasar da ake kira "Futa Jallon".

Babu ko shakka, akwai taqaddama akan wannan fahimta domin Zuri'ar Sheikh Danfodiyo dai sun zo ne daga Qasar Futa Toro da ke cikin kwarin Kogin Senegal **(River Senegal Valley).** Asalin su na Futa Toro ya sa ake kiran su FULANI TORONKAWA. Kuma Zuri'ar Sheikh Shumo sun zo ne daga Qasar Futa Jallon wadda ke a bisa Tsibirin Djallon **(Futa Djallon Highlands**) da ke Qasar Guinea. A nan ina kyautata zaton wannan Zuri'a ta Sheikh Shumo suna cikin tsatson FULANI JALLOW ko kuma JALLOH. To, yanzu dai akwai Fulani Toronkawa daga Toro, Dallazawa daga Dallaje, Sulluvawa daga Sulluve; ashe qila sai a samo JALLAWA daga Jalloh!!!

Wani littafi mai suna "A Short History of West Africa AD 1000-1800" na T.A. Osae da S.N. Nwabara wanda aka wallafa a Ingila (1968); ya bayyana cewa Zuri'ar Sheikh Danfodiyo sun zo Qasar Hausa tun Qarni na 15, watau wajejen 1480 AD. Amma wasu marubuta sun fi dogara da cewa Zuri'ar Shehu Danfodiyo sun zo Qasar Hausa ne wajejen shekarar 1680 AD bayan

Zawiyyar Sheikh Nasir Ad-Deen ta Mauritania ta qaddamar da Jihadi har zuwa Futa Toro a 1650 AD inda Fulani Torodbe suka taimaka masa, amma Jihadin ya ruguje a shekarar 1677 AD. Wannan ya sanya Fulani suka watse zuwa wasu sassa na Afirka ta Yamma. Wannan riwaya ce ta Richard Gray a cikin "The Cambridge History of Africa (1975)". Wasu masana Tarihi kuma suna ganin cewa Sheikh Usman Danfodiyo ya samo zimmar yin Jihadi ne daga Qasar sa ta Asali, watau Futa Toro, lokacin da ya samu bayanin cewa Fulani Torodbe mabiya Sheikh Sulayman Bal sun yi Jihadi kuma sun amshe Qasar Futa Toro daga hannun Zuri'ar Denianke a shekarar 1776 AD. A wannan lokaci ne aka kafa Daular Futa Toro wadda ake kira **"Imamate of Futa Toro**" ko kuma **"Caliphate of Futa Toro**", wadda babu irinta a duk faxin Afirka ta Yamma a wancan lokacin. Wannan bayanin yana cikin "Encyclopaedia of African History (2005)".

Kamar yadda aka yi ittifaqi, Zuri'ar Sheikh Muhammadu Shumo sun zo ne daga Futa Jallon kuma sun zauna a Birnin Sifawa kamin su zo Qasar Katsina inda suka zauna a Garin Makurxa kamin su koma cikin Birnin Katsina. To, amma xan gajeren tarihin da muka bayar a sama na Zuri'ar Sheikh Danfodiyo ya tabbatar da cewa ba tare suka zo Qasar Hausa ba da Zuri'ar Sheikh Shumo. Kuma asalin su ba daga Qasa guda su ke ba domin Qasar Futa Toro da Qasar Futa Jallon daban-daban su ke; duk da yake mazauna wuraren biyu yawancin su Fulani ne daga tsatso iri daban-daban.

Jihadin Fulani na Futa Toro a 1776 AD da na Fulani magoya bayan Sheikh Usman Danfodiyo a Qasar Hausa a 1800 AD, duk sun samo zimma ne daga Jihadin farko na Fulani a Qasar Futa Jallon wajejen shekarar 1700 AD wanda ya sanya aka

samu cikakkar nasara a shekarar 1725 AD. Wannan Jihadi shi ne na farko da Fulani suka qaddamar a faxin Afirka ta Yamma kaf; kuma an yi shi ne a qarqashin jagorancin Sheikh Karamokho Alfaya wanda galaba a yaqin Talasan ya tabbatar da shi. Bayan rasuwar Sheikh Alfaya a 1751 AD sai Sheikh Ibrahim Soriya ya hau gado. Sheikh Soriya ya rasu a 1791 AD; wanda rasuwar sa ta kawo rikici a Daular har ta yi rauni. Daga baya aka daidaita tsakanin Zuri'ar Alfaya da Zuri'ar Soriya suka riqa karva-karva wajen shugabancin Daular.

Daulolin Futa Jallon da na Futa Toro sun haxa kansu suna mulki a wancan yanki na Afirka. Tun da dama bakin Tekun Atlantic su ke, sai suka shiga cinikin Bayi da saida dabbobi da kayan gona ga Mutanen Faranshi da Mutanen Portugal. An daxe ana yin waxannan cinikayya har zuwa 1896/1900 lokacin da Turawan Ingilishi da na Faransa suka amshe mulki a Futa Toro da Futa Jallon kamar yadda suka yi a sauran wurare na Afirka har da Daular Usmaniyya ta Sakkwato.

A bisa dukkan alama, Zuri'ar Sheikh Shumo, watau iyayen sa ko kuma kakaknin sa, sun shigo Qasar Hausa ne kamin ko kuma daidai lokacin Jihadin Futa Jallon wajejen shekarar 1700 AD. A bisa yadda ake tafiye tafiye wa wancan lokacin, za'a iya tabbatar da cewa wanda duk zai zo Qasar Hausa daga Afirka ta Arewa ko ta Yamm, ko ta Gabas, to, lallai ya biyo ta cikin Daular Kanem-Bornu wadda babu irin ta a duk faxin Afirka a lokacin. Ashe za'a iya cewa Zuri'ar Sheikh Shumo sun biyo ta Babban Birnin Daular Borno, watau Ngazargamu wanda babu Birni mai girman sa a lokacin a duk Afirka baya ga Alqahira (Cairo). Wata qila a can ne suka samu labarin Birnin Sifawa wanda aka tabbatar da cewa Kanuri ne daga Zuri'ar SAYFAWA na Bornu suka kafa ta domin ilmatar da Hausawa Addinin

Musulunci. Kuma Birni ne wanda babu kamar sa a Qasar Gobir ko Qasar Zamfara a wajen Ilmin Addinin Musulunci a wancan lokacin. Wannan ya sa Zuri'ar Sheikh Shumo suka zo Birnin Sifawa inda wata qila daga baya suka haxu da Zuri'ar Muhammad Danfodiyo mahaifin Sheikh Usman Danfodiyo. Daga nan sai a kyautata zaton cewa Sheikh Muhammadu Shumo ya jagoranci Zuri'ar su zuwa Yandoto wanda shi ne Birni mafi daraja wajen Addinin Musulunci a Qasar Katsina Laka a wancan lokacin. Dagan nan ne suka tafi zuwa babban mazauninsu a Makurxa a shekarar 1750 AD.

## RUFEWA

Mai Girma Shugaban Taro,

Zuri'ar Hambalawa,

Littafin ku mai suna "THE HAMBALI CLAN" wanda Gambo Ibrahim Maigari da Pharm. Ahmadu Ibrahim Maigari da Mustapha Ahmed Ibrahim suka wallafa, ya bayar da isashen bayani daga wannan shekara ta 1750 har ya zuwa zamanin mu na yau a kan ayyukan alheri da Zuri'ar ku ta yi, kuma ta ke yi ba. Don haka ba sai na nanata ayyukan alheri da Zuri'ar ku ta yi ba a Qasar Hausa da kuma Qasar Katsina da ma Najeriya baki xaya.

Sai dai akwai wani abu Muhimmi da Littafin naku da sauran rubuce-rubuce da aka yi game da ku ba'a ambata ba. Wannan shi ne cewa **ZURI'AR KU TA ALQALAI DA LIMAMAI** a Qasar Katsina; suna cikin masu Zavar Sarkin Katsina kamin da kuma lokacin Turawa. Har yanzu ba'a gane dalilin da ya sanya da Babban Alqali da Babban Liman suka vace daga cikin masu Zavar Sarki ba a Katsina. Tabbacin wannan ya zo a cikin bayanin:

National Achives Kaduna File No. NNAK/KATPROF/1670,1926

A cikin wanna File na National Achives an jera sunayen masu Zavar Sarki a Katsina xaya na bin xaya kamr haka:

1. Durvi
2. Qaura
3. Galadima
4. Marusa
5. Sarkin Gabas
6. Iya
7. Alqali

A cikin Littafin Dr. Yusuf Bala Usman (1968), ya lissafa masu Zaven Sarki a Katsina xaya na bin xaya kamar haka:

1. Sarkin Sulluvawa
2. Yanxaka
3. Qaura
4. Galadima
5. Durvi
6. Liman
7. Sauran Fitattun Mutane

Ina godiya da kuka bani dama na faxi xan abinda Allah Ya sanar da ni game da Zuri’arku da abin da ya shafi haka.

Da fatan zaku zurfafa bincike a kan Zuri’ar ku domin fitar da ingantaccen Tarihi da zaku qara gamsuwa da shi, nake cewa,

**Wassalamu Alaikum wa Rahmatul Lah**